Lallai cewa wani Bayahude ya zo wajen Annabi sai ya ce da shi ya muhammad, Cewa Allah ya rike Sammai kan Yatsa daya, Kuma Kassai Kan Yatsa daya, kuma Duwatsu kan Yatsa daya, kuma Bushiyu Kan Yatsa daya, Kuma Halittu kan Yatsa daya, sannan ya ce: Ni ne Sarki

An rawaito daga Abdullahi Bn Masud -Allah ya yarda da shi: Lallai cewa wani Byahude ya zo wajen Annabi sai ya ce da shi ya muhammad, Cewa Allah ya rike Sammai kan Yatsa daya, Kuma Kassai Kan Yatsa daya, kuma Duwatsu kan Yatsa daya, kuma Bushiyu Kan Yatsa daya, Kuma Halittu kan Yatsa daya, sannan ya ce: Ni ne Sarki
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Wannan Hadisin yana nuna girman Allah -Madaukaki- yada ya sanya sammai baki dayan su akan Dan yatasa daya daga cokin Yan yatsun Masu girma da Karamci, kuma ya kidanye Halittu sanannu ga Halitta da kuma girmansa da Daukaka, kumaya bada labari cewa kowane nau'i daga cikin su -yana sanya shi- akan Danyatsa daya, da kuma Allah yaga dama da ya sanya sammai da kassai da abunda ke tsakaninsu a kan Dan yatsa daya daga cikin Yan Yatsun Hannunsa -Mai girma da daukaka- kuma wannan yana daga cikin Ilimin da aka gada daga Annabaw, wanda aka karbo shi ta Hanyar Wahayi daga Allah -Madaukakin Sarki- saboda haka Manzon Allah ya gasgata Maganar bayahude kai yayi mamakin ta har yayi farin ciki da ita, shi yasa yayi Dariya kar aka ga firorinsa, don gasgata shi Kamar yadda Abdullahi Bn Mas'ud ya ce: a cikin wata Riwaya daban daga gare shi, juma Aannabi ya Karanta fadin Allah Madaukakin Sarki: "Basu girmama Allah ba Matukar girmamawa kuma Kasa tana tana damkinsa a Ranan Al-kiyama kuma Sammai suna nannade a Hannun gamansa tsarki ya tabbata ga Allah kuma ya daukaka game da Abunda suke masa shirka da shi" wacce akwai tabbatar da Hannaye ga Allah Madaukakin Sarki, saboda tabbaraewa da abin da bayahude ya ce: kuma ko kallo bai isa ba abunda wadanda suke Musanta Siffofin Allah, ya kore sifar Yatsu ga Allah, yana mai rayawa cewa tabbatar da ita ga Allah siffata shi ne da Halittarsa, kuma bap sani ba wannan Mai Musun Siffofin Allah cewa tabbatar da wannan cewa tabbatar da siffofin Allah baya nuna Kamanceceniya, kamar yadda cewa Mu muna tabbatar Masa da Rayuwa da iko da Karfi da kuma ji da gani, kuma hakan baya nuna cewa Kamanceceniya da Haliiarsa, saboda shi Allah Madaukakin Sarki "Babu wani abu Kwatankwacinsa kuma shi mai ji ne Kuma Masani"